(١)

## KAYAYYAKIN GWAMNATI TSAKANIN GIRMAMA AMFANA DA SU DA KUMA HATSARIN LALATA SU

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Shi ne ya farar da halittarku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ta)** [Hudu: 61]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai addinin Musulunci, addini ne na gini da raya ƙasa, addini ne na nagarta da gyara, dukan saƙwannin da suka zo daga Allah Maɗaukakin Sarki suna kira ne zuwa ga waɗannan manyan ƙa'idoji, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Annabi Musa (AlaiHis Salam) ya ce wa ɗan uwansa, ka wakilce ni a cikin mutane na, ka yi gyara, kada ka bi hanyar maɓarnata)** [al-A'araf: 142], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi ta bakin Annabi Shu'aib (AlaiHis Salam) cewa: **(Ni fa babu abin da na nufa banda yin gyara daidai gwargwadon iyawa ta, samun dacewa ta tana wurin Allah; gare shi kaɗai na dogara, kuma wurinsa nake komawa)** [Hudu: 88].

Babu shakka kiyaye kayayyakin gwamnati, waɗanda mallaki ne na al'umma, wanda gwamnati take aiki wajen cigabansu, da kuma inganta su, ta yanda za su amfani ɗaukacin al'umma, ganin cewa haƙƙin amfana da su ba mallakan wani mutum shi kaɗai ba ne, ba kuma na waɗansu 'yan tsirarun mutane ba ne, a'a haƙƙi ne

na gaba ɗayan al'umma; saboda haka, kaman yanda mu duka ne muke amfana da su, to kuwa tilas ne mu kiyaye su gaba ɗayanmu, mu kuma hana maɓarnata yin kowane irin yunƙuri da suke yi na ɓata su, da hana su gabatar da hidimar da aka yi su saboda su.

Wajibi ne ga duk wanda aka ɗaura masa alhakin gudanar da kayayyakin gwamnati, ya gabatar da aikin da aka ɗaura masa saboda Allah, da kuma kyautata aikin, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Allah yana son idan wani daga cikinku zai yi wani aiki ya kyautata shi),** haka ma shi ma wanda zai amfana da aikin, to ya yi amfani da shi ta hanyar da ba zai kai zuwa ga cutarwa, ko lalata shi, ko yin ɓarna da shi ba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Babu cuta babu cutarwa),** da haka ne za a sami tabbacin yin taimakekeniya tsakanin dukan ɓangarori da sassan al'umma akan alhairi da amfanin gaba ɗayan al'umma, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: (**Ku yi taimakekeniya akan biyayya da tsoron Allah, kada ku yi taimakekeniya akan aikata zunubi da saɓo da zalunci)** [al- Ma'ida: 2].

Lallai kiyaye kayayyakin gwamnati wajibi ne da shari'a ta wajabta, kishin ƙasa, da mutuntaka kuma suka ƙarfafa, wannan wajibi bai kawai taƙaita da kiyaye kayan daga lalacewa ba, a'a, ya wuce haka har zuwa yin aiki tuƙuru wajen ƙara yawan amfanar da ake yi da su, da cigaba da su, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa**: (Abubuwa guda bakwai ladansu suna isa zuwa ga bawa har lokacin da yake cikin kabarinsa, bayan ya yi rasu: wanda ya karantar da ilimi, ko ya jawo kogi, ko ya haƙa rijiya, ko ya dasa dabino, ko ya gina Masallaci, ko ya**

**gadar da Alƙur'ani, ko ya bar ɗa da yake nema masa gafara bayan rasuwarsa).**

Abin da (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake nufi da **(ko ya jawo kogi)**, shi ne: ya ƙara faɗaɗa shi, kuma ana yin ƙiyasi da wannan wajen faɗaɗa duk wata magudana ta ruwa, dole ne mu tsaftace su, mu kuma faɗaɗa su, ba wai mu gurɓata su, ko mu ƙara taƙure su ba, haka ma al'amarin yake game da hanyoyin gwamnati da al'umma ne suke amfana da su, wajibi ne mu kyautata kiyaye su, ba wai mu lalata su, ko mu taƙure su, mu hana masu wucewa su wuce ta kansu, ko mu rinƙa jefa shara da dagwalo da makamantansu ba.

Duk wanda ba shi da iko ƙara amfanin da kayayyakin gwamnati suke yi wa al'umma, to ya kamata ya yi aiki wajen kwaɗaitar da waɗanda suke da ikon yin haka, saboda ya yi aiki da maganar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da yake cewa: **(Duk wanda ya shiryatar wajen aikata aikin alhairi, daidai yake da wanda ya aikata a aikace)**, idan kuma bai iya yin haka ba, to ya kame hannunsa daga ɓarnata komai daga ciki, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Allah ba ya son maɓarnata)** [al- Ma'ida: 64], haka ma Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Lallai Allah ba ya son maɓarnata)** [al- Ƙasasi: 77], haka ma dole ne mu yi aiki gaba ɗaya wajen kiyaye su, da kuma kyautata amfana da su.

Muna ƙara tabbatar da cewa lallai dukan kayan gwamnati mallakin ɗaukacin al'umma ne, irinsu: hukumomi, da makarantu, da asibitoci, da hanyoyi, da kayayyakin sufuri, dukansu amana ne da Allah zai yi mana hisabi akansu, bai halatta mu yi sakaci ko wasa da su ba, bai kamata mu lalatu, ko mu yi ganganci wajen amfani da su ba.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Babu shakka kiyaye kayayyakin gwamnati, da rashin ɓarnata su, ɗaya ce daga cikin hanyoyin alhairi, da hanyoyin samun tsira da rabo, saboda haka ne Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya sanya rashin cutarwa a matsayin wani kaso ne a cikin imani, kuma ɗaya daga cikin nau'o'in sadaka, kuma sanadi ne na shiga aljanna, mai tsira da aminci yana cewa: **(Imani ya kasu zuwa gida saba'in da wani abu ne, ko sittin da wani abu, mafi girman kason shi ne faɗin "La'ilaha illalLahu", mafi ƙanƙantarsa kuma shi ne kawar da abu mai cutarwa daga hanyar bin mutane),** haka ma mai tsira da aminci yana cewa: **(Musulmi na gaskiya shi ne wanda mutane suka kuɓuta daga sharrin harshensa da na hannunsa),** haka ma mai tsira da aminci yana cewa: **(Lallai na ga wani mutum yana kai- komansa a cikin aljanna; sakamakon sare wata bishiya da ya yi da take tsakiyar hanyar bin mutane, tana cutar da Musulmai)**, haka ma mai tsira da aminci yana cewa: **(Ka kame sharrinka ga barin mutane ma sadaka ne da kake yi wa kanka).**

Lallai muna matuƙar buƙatar wayar wa da al'umma da kai game da muhimmancin kayayyakin gwamnati, da wajibcin ba su kariya; ta hanyar dasa tsarin ɗaukan alhaki wanda addini, da zamowa ɗan ƙasa na gari suka shiryatar, domin bai wa ƙasa kariya, da kiyaye kayayyakinta, da kuma haɓaka tattalin

arzikinta, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Duk wanda ya ji tsoron Allah, ya kuma gyara abin da ya ɓata, to kuwa babu wani tsoro a gare su, ba kuma za su yi baƙin ciki ba)** [al- A'araf: 35].

**Ya Allah ka kare mana ƙasarmu da sauran ƙasashe.**